# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kwallon ƙafa salon Afirka
## Kashi na uku: Kwallon ƙafa mai launin fari da baƙi


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya tace: | Ludger Schadomsky da Maja Braun |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| John: | ɗan shekara 15 |
| Honourable Gambo: | ɗan shekara 55 |
| Metogba: | ɗan shekara 28 |
| Zakari: | ɗan shekara 14 |
| Shehu: | ɗan shekara 14 |
| 'Yar jarida: | 'yar shekara 25 |

**MAI GABATARWA**:

Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu". A shirin da ya gabata, Safina ta kusa fid da rai a burinta na ta ci gaba da buga wasan ƙwallon ƙafa, saboda antinta ta ƙi yarda da wannan magana. Sannan shi kuma Honourable Gambo, ya nemi ya sadu da ɗan wasan ƙwallon ƙafan nan da ke da niyyar shirya wata gasa a birnin Gabas. Sannan wai shin, Zakari zai sami damar shiga gasar kuwa? Sai ku biyo mu domin jin yadda al'amarin zai kasance**.** Yau za mu fara shirin ne daga inda Honourable Gambo ya je ganin ƙwararren ɗan wasan nan a otel ɗinsa.

**Fitowa ta 1: A otel**

John, Honourable Gambo, Metogba

**HON. GAMBO:** Barka dai! A'a! Kai dakata! Wa nake gani haka? Metogba! Allah mai iko! Abin ya ba ni mamaki.

**METOGBA:** Sannunku dai. Ina ganin kai ne baƙon ko? E, ni ne Metogba. Kuma na ga alama ka san haka. Kai kuma fa?

**HON. GAMBO:** Gambo, sunana Honourable Gambo. Ɗan majalisa mai wakiltar mazaɓar birnin Gabas. Na ji daɗin saduwa da kai, Metogba! Ban taɓa tsammanin cewa ƙungiyar shirya wasan ƙwallon ƙafa ta ƙasarmu za ta gayyaci ɗan wasa kamarka ba, da ya yi suna a duniya. Af, har na kusa mantawa, Metogba, wannan ɗana ne, John.

**JOHN:** Ba..ba..barka kadai.

**METOGBA:** Barka dai John. To Mr. Gambo, me ke tafe da kai? Kamar yadda ka sani, akwai abubuwa da dama da za mu yi kafin a fara gasar, amma kuma ba lokaci sosai, duk dai da manufa mai kyau ce: zaman lafiya da kawo daidaito a ƙasarmu.

**HON. GAMBO:** Ba damuwa! Ba damuwa, Metogba, ba zan ɓata maka lokaci ba. Ɗana John masoyinka ne matuƙa. Ni ma haka. Na ji labarin cewa ƙungiyar da za ka zaɓa ta matasa goma sha ɗaya, za ta je ƙasar Turai don buga wasannin sa da zumunta.

**METOGBA:** Wannan haka yake.

**HON. GAMBO:** Yauwa! To tunanina…uhmm…ina tunanin cewa ko... Abin da nake buƙata shi ne, ka taimaka ka ba John damar shiga wannan ƙungiyar, Metogba. Ya iya wasa sosai, kuma yana da burin ganin cewa ya yi nasara a wasan ƙwallon ƙafa kamarka, Metogba.

**METOGBA:** Mr. Gambo, idan na fahimce ka, wato kana nufin in shigar da yaronka tun kafin ma a fara gasar, haka ne?

**HON. GAMBO:** Yauwa! Yauwa, Metogba! Ka ba yaron dama kawai. Za a saka maka sosai.

**METOGBA:** Yallaɓai, wannan abin ba zai yiwu ba. Ka san wasan ƙwallon ƙafa, wasa ne wanda ba cutarwa a cikinsa. Ka tura yaronka wurin gasar kamar sauran yara. In ya cancanta, zan ɗauke shi. Dangane da kuɗinka kuwa ko wata kyauta, ina so ka san cewa, ni da ƙungiyata, za mu ɗauki nauyin duk abin da za a kashe na yaran nan guda goma sha ɗaya, a yayin da suke ƙasar Turai. Saboda haka in har kana so ka taimaka ne, to ka miƙa gudummuwarka ga gidauniyar ƙungiyar. Na gode, kuma na bar ka lafiya.

**HON. GAMBO:** Tsaya mana, Metogba! Ba ka ganin ya kamata dai mu ƙara tattaunawa game da wannan?

**METOGBA:** Yallaɓai, ka manta da wani abu ɗaya. Ni ɗan ƙwallo ne fa, ba ɗan siyasa ba.

**MAI GABATARWA:**
Honourable Gambo dai bai tsammaci zai samu irin wannan amsa ba.Ya saba samun biyan buƙata ta kowace irin hanya. Wannan zai tsai da shi? A gidan abinci kuwa, Shehu da Zakari na kammala tattaunawar da suke yi. Bari mu saurare su.

**Fitowa ta 2: A gidan abinci**
Zakari, Shehu

**ZAKARI:** To Shehu, me kake gani? Muna iya gwadawa mu gani? Mai karanta labarun ya ce yara masu shekaru daga goma sha biyu zuwa goma sha shida za su iya zuwa wurin gwajin. Ni yanzu shekaruna goma sha huɗu. Kai fa?

**SHEHU:** Zaks! Lalle haukar da kake yi ta wuce yadda nake tsammaninta. Dube ka, dube mu! Wa kake ganin cewa zai ba mu damar shiga gasar da za a yi? Kuma idan ma sun yi, ka san cewa da zarar sun san inda ka fito, haka za su ajiye ka kamar wani dankalin Turawa mai zafi.

**ZAKARI:** Haba da Allah, me ya haɗa yarena da wasan ƙwallon ƙafa? Da ƙafafuwana nake wasa fa, ba da harshena ba!

**SHEHU:** Haka ne? Ai sai ka gaya wa mai horas da 'yan wasan ƙungiyarmu ta ƙasa, tun da duk 'yan ƙungiyar ai yarenshi ne. Ka manta kawai Zakari. Kaddara ta riga fata, mu a kan titi za mu yi rayuwarmu har ta ƙare.

**ZAKARI:** Amma Shehu, wannan gasar zaɓen fa na ƙarƙashin jagorancin wani ƙwararren ɗan wasa ne fa daga wata ƙasa. Ba zai damu da yaren da nake yi ba, ko kuma ni almajiri ne.

**SHEHU:** Kai sai ka riƙa magana kamar kai baƙo ne a birnin Gabas. Da kai da ni mun san cewa, sun riga sun gama zaɓen waɗanda suke so, saboda haka wannan gasar zaɓen da za a yi, don dai kar a ce ba a yi ba ne kawai. Na ji cewa ni almajiranci nake yi, amma ni ba sakarai ba ne.

**SHEHU:** Ina ganin maganar gaskiya ce. Ba zan sami dama ba. Wannan ɗaya ne daga cikin irin mafarke-mafarkena, wanda ba zai taɓa zama gaskiya ba. Kamar yadda nake mafarkin gane su wane ne iyayena. Na sadaukar.

**SHEHU:** Haba Zaks, ai muna tare, ko ba haka ba ne? Ka zama namiji mana. Yanzu kuma ina za ka?

**ZAKARI:** Ba ko'ina. Ni ai taƙure min.

**SHEHU:** Ba ka manta da wani abu ba? Kwallonka, ungo! Kama, ga ta nan!

**MAI GABATARWA:**

Zakari ya ɗauki ƙwallonshi, sannan ya nutsa cikin lungunan birnin Gabas, yana cikin juyayi da yin da-na-sani da abin da Shehu ya faɗa masa. Kana tunanin cewa da ya yi biris da shawarar da Shehu ya ba shi? A lokacin da zakara farko ya yi cara, sai fa ya farka, ya ɗauki ƙwallonshi, sannan ya wuce zuwa filin wasan da ya saba zuwa yana wasa. Bai san cewa wannan shi ne abin da zai canza mishi rayuwa kwata-kwata ba. Amma yanzu, bari mu koma wajen 'yan jaridu, inda suke jiran Metogba, don ya gudanar da jawabin da zai yi musu a otel ɗin da ya sauka.

## Fitowa ta 3: Taron 'yan jaridu a otel

'Yar jarida, Metogba

**'YAR JARIDA:** Yauwa, ga shi nan zuwa!

**METOGBA:** Jama'a, barkanku da warhaka. Yanzu ina ganin kamata ya yi mu ci gaba da abin da ya tara mu a nan ko? Ina sauraron tambayoyinku.

**'YAR JARIDA:** Metogba, ta yaya kake ganin wasan ƙwallon ƙafa zai kawo zaman lafiya da daidaito a wannan ƙasa tamu? Kuma mene ne dalilin yin wannan gasar?

**METOGBA:** Na'am, uhm… don Allah ko akwai ƙwallo a nan kusa? Yauwa, na gode. Yanzu wace kala ce wannan ƙwallon?

**'YAR JARIDA:** Baƙi da fari.

**METOGBA:** Haka yake! To yanzu mu yi tunanin cewa, kalar wannan ƙwallon su ne manyan yarurruka guda biyu da muke da su a ƙasar nan. Kalolin ƙwallon nan daidai suke, ba inda suka saɓa da juna. A gaskiya ma sun dace da juna sosai, ta yadda idan aka sace iskar wannan ƙwallon… gaba ɗaya iskar za ta fita. Ba wai ɓangaren baƙin, ko farin ba. Kwallon ce gaba ɗayanta za ta sace. Sannan idan kuma muka ƙara mai da iskar… don Allah a miƙo min abin sa iskar nan. Yauwa, na gode! … Kun gani, tare ƙwallon take tashi, da kalolin a lokaci ɗaya. Saboda haka, dalilin shirya wannan gasar shi ne, don in taimaka wajen haɗa kan jama'ar wannan ƙasa, sannan kuma in zaƙulo yara 'yan wasa masu hazaƙa, waɗanda za su yi fice a harkar wasan ƙwallon ƙafa a duniya.

**'YAR JARIDA:** Akwai labaru da zato da ake yi cewa, tuni ƙungiyar shirya

wasan ƙwallon ƙafa ta ƙasa ta zaɓi waɗanda ake so. Me za ka ce dangane da waɗannan jita-jita?

**METOGBA:** Abin da zan ce kawai game da wannan shi ne, jita-jita ce kawai. Cin hanci da nuna son kai ya ɓata harkar wasan ƙwallon ƙafa a nahiyar Afirka. Amma ina ba duk masu sha'awar wasan ƙwallon ƙafa a ƙasar nan tabbacin cewa, zan ba kowane ɗan wasa hakkinsa, kuma ba zan yi zalunci ba wajen zaɓen wanda ya fi cancanta, saboda na san zafin nuna bambanci saboda kalar mutum, ko yarensa, ko kuma shi ɗan wane ne, ko saboda addininsa, ko don shi namiji ne ko mace.

**'YAR JARIDA:** Me za ka ce dangane da takaddamar da aka saba yi a kan wasan ƙwallon ƙafa tsakanin gwamnatin ƙungiyoyin shirya wasan ƙwallon ƙafa a yawancin ƙasashen Afirka?

**METOGBA:** Ina ganin ya kamata a ce 'yan ƙwallo ne kawai ya kamata su riƙa tafiyar da harkokin wasan ƙwallo, ba 'yan siyasa ba. Mun san cewa yawancin 'yan siyasarmu, in ba son zuciyarsu ba, ba wani abu da ya dame su. Ba su cika damuwa da biyan buƙatun 'yan wasa ba. … Ba wasan da ya kai wasan ƙwallon ƙafa kawo kuɗi a duniya. Sannan idan aka tafiyar da shi yadda ya kamata, to zai iya kawo kuɗin shiga masu yawa ga ƙasar. Samun damar ɗaukar nauyin gudanar da wani babban wasan ƙwallon ƙafa, kamar gasar cin kofin nahiyar Afirka, ko na cin kofin duniya, wata dama ce, ba ga 'yan wasan ƙasar da za ta ɗauki nauyin ba kawai, har ma ga ƙasar baki ɗaya, na ta inganta harkokin rayuwarta, sannan ta ƙirƙiro da hanyoyin samun aiki.

**'YAR JARIDA:** Metogba, mun gode da ka sami halartar wannan ganawa tamu.

**METOGBA:** Ba damuwa. Ni ma na gode.

**’YAR JARIDA:** Metogba! Ko za ka yi min wata alama a nan, don Allah?

**MAI GABATARWA:**
A lokacin da aka kammala taron ’yan jaridun, kuma Metogba ya fita daga otel ɗin, shi kuma Zakari na tsaye shi ɗaya da ƙwallonshi ta tsumma a filin da yake wasa.

**Fitowa ta 4: A filin wasa**
Zakari

**ZAKARI:** Yauwa! Yanzu bari in gani. Kwallo a ƙasa, taku goma baya: ɗaya, biyu, uku, huɗu, biyar, shida, bakwai, takwas, tara, goma. Ko kuma, bari in ƙara ɗaya, ya zama goma sha ɗaya ke nan. Yauwa! Yanzu bari in gani ko za ka iya kama wannan ƙwallon daga kai sai tsaron gida. … Uhm … Wayyo Allah! Yanzu me ja wa kaina? Me kuma na yi haka?

**MAI GABATARWA:**
Fashewar gilashin tagar nan ya sa Zakari tunanin abu ɗaya, cewa shi ma tashi ta ƙare. Haka ma duk wani tunanin da yake yi na ya zama wani abu. Amma haka ne? Tagar wane ne ya fasa? Kuma me zai biyo bayan wannan ta’asa? A can kuma wurin da za a gudanar da gasar, wane irin ƙalubale ne Metogba zai fuskanta a ƙoƙarinshi na haɗa ƙungiyar? Sai ku kasance da mu a shiri na gaba, don jin abubuwan da za su biyo baya. Kuna iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo domin sake sauraro ko aiko da tsokaci. Adireshin kuwa: www.dw world.de/lbe.